
# MAGAMA

Nuwamba 2005 Shaaban 1426 Kyauta



## Taimakon Kai-da-kai Shi Ne Tushen Arziki Mai Dorewa

ISSN 0794-0262

## Ziyarar Ambasada John Campbell Zuwa Jihar Sakkwato A Cikin Watan Ramadan.



Mai Girma Gwamna Sakkwato, Alhaji Attahiru Bafarawa ya ba da kyauta ga Ambasada John Campbell a lokacin ziyararsa a Jihar Sakkwato



Ziyarar ban-girma ga Mai Martaba Sarkin Musulmi, Alhaji Muhammadu Maccido.



Cin abincin buɗa-baki tare da Mai Martaba Sarkin Musulmi a faɗarsa da ke Sakkwato.



Mai Girma Wazirin Sakkwato, Dokta Usman Junaidu na karanta mujallar *Magama.*


## Shirin Buɗa-baki Na Ofishin Jakadancin Amirka Tare Da Kungiyar Al-habibiyya



Hajiya Rukayya Iliyasu, Amirah ta Kungiyar Al-Habibiyya na bayanin wannan shiri ga Jami'an Ofishin Jakadancin Amirka.



Ɗimbin jama'a sun halarci wannan shiri sun kuma yaba ma waɗanda suka ɗauki nauyinsa



Aikin ƙauna da nuna tausayawa ga marasa ƙarfi babbar al'ada ce ga Amirkawa



Jami'an Ofishin Jakadancin Amirka na ƙoƙarin raba abinci ga mabuƙata

MAGAMA

Oktoba/Nuwamba 2005 | Jimada Akhir 1426 | Kundi Na 1, Fitowa Ta 20

# Muna Kaunar Dangantakarmu Da Nijeriya



Zuwa ga Jama'ar Magama: Watan Nuwamba a Kasar Amirka yana da muhimmancin gaske.

A watan ne muke tunawa da Tarihin Gargajiyar Amirka, mu kuma tuna da girmama irin sadaukar da rayukan da tsofaffin sojojinmu suka yi, kazalika da bayar da hutun yin addu'o'i. Yin addu'o'i wata hanya ce ta nuna godiyar da ke cikin zukatan ɗan Adam.

Kwanan nan, Ambasada Campbell yake tuna wa waɗansu manyan shugabannin Nijeriya cewa, mu a Amirka muna matuƙar girmama dangantaka. Muna ma da wani karin maganar da ke cewa: "abokinka masoyinka ne."

Lokacin kuma da muke ta fama da bala'in da guguwar Katrina da Rita suka yi mana, jama'ar Nijeriya sun jajenta mana, sun kuma nuna damuwa, a inda suka yi addu'o'i da tara kuɗaɗe don bayar da agaji. Ba za mu taɓa mantawa da wannan alheri ba.

Sabuwar Mataimakiyar Sakatariyar Gwamnatinmu kuma, mai kula da Harkokin Afirka, Dokta Jendayi Frazer, ta ziyarci Nijeriya (Duba Shafi Na 16). Kafin ma ta yi wani jawabi, sai da Ambasada Campbell ya jagorance ta da sauran ma'aikatan ofishin jakadancinmu, don yin shiru na minti ɗaya, na girmama Uwargida Stella Obasanjo, wadda ta mutu a Kasar Span, da kuma waɗanda suka rasa rayukansu, a haɗarin jirgin saman Kamfanin Bellview. A duk lokacin da jama'a suka jajenta wa juna a kan ƙara samun danƙon zumunci.

'Yan Nijeriya da Amirkawa sun yi girmamawar ƙarshe ga abokin aikinmu, Manjo Joseph Haydon. Kai har da ma jama'ar yankunan karkara da ba su ci moriyar Manjo Haydon ba, a matsayinsa na Babban Jami'in Tsaro na Hukumar (ODC). Sun bayyana shi da cewa mutum ne mai hali na gari da jarumtaka. (Duba Shafi Na16).

Kasar Amirka kuma ta yi jana'izar Misisi Rosa Park. Uwa ga dukan harkokin neman 'yancin ɗan-Adam, a wannan zamanin. Mace mai kamar maza. Misisi Park ce ta fara yin ƙememen barin a yi zalunci, ta kuma kaɗa kugen da ya daidaita halayyar Amirkawa. Wannan jaruntaka tata ce ta ƙarfafa mana mulkin dimokuraɗiyya.

A wannan fitowar ta *Magama*, mun bi sahun takwarorinmu 'yan Nijeriya, don yin godiya ga Shirin Jakada na Taimakon Kai-da-kai da rashin nuna bambanci. A fannin tallafa wa zawarori kuma Ofishin Jakadancin Amirka a Nijeriya ya bai wa ƙungiyoyin yankuna karkara tallafin yin sana'o'in da za su inganta rayuwarsu.

A tambayi Limamiyar Kirista, Mary Joseph Uzoigwe, da ke Ikpa Mbeke, a Jihar Imo mana. Kauyen da yanzu ke da tsabtataccen ruwan sha.

A wajen godiya ma Limamiyar Kirista Uzoigwe cewa ta yi, "lafiya uwar jiki" (Duba Shafi Na 3).

Muna godiya ga jama'ar *Magama*, game da imaninku. Allah ya karɓa, Amin.

*Atim Eneida George*
Naku, 'Yar Asalin Duniya

MA'AIKATAN MUJALLA

CLAUDIA E. ANYASO
Jami'ar Hulɗa Da Jama'a A Nijeriya

RUDOLPH E. STEWART
Jam'in Labarai

SANI MOHAMMED
Edita

ISHAKA ALIYU
Mai Ba Da Shawara Game Da Wallafawa

Ofishin Jakadancin Amirka ke wallafa wannan mujallar kowane wata. A aiko da wasiƙu zuwa ga
Sashen Hulɗa da Jama'a, Lamba 1075 Titin Difulomasiyya, Tsakiyyar Gari, akwatin gidan waya mai lamba: 5760, Abuja, Nijeriya.
09-4614000 Fax: 09-4614011. Ofishin na Legas: akwatin gidan waya mai lamba: 554, Legas.
Tel: 01-2632577, 2633560, 2633395. Na'urar INTERNET: http://nigeria.usembassy.gov/wwwhmagama.html

# Kungiyoyi 13 Sun Amfana da Shirin Taimakon Kai

Buri ya cika! A ranar 29 ga watan Satumbar 2005 ne, ƙungiyoyi 13 suka amfana da tallafin Dalar Amirka dubu 140 na Shirin Jakadan Amirka a kan Harkokin Taimakon Kai Da Kai (SSH) da kuma Shirin Ribar Mulkin Dimokuraɗiyya da 'Yancin Ɗan Adam (DHRP).

Wannan tallafin ya taimaka ga aiwatar da ayyuka a yankunan jama'a da dama. Ayyukan sun haɗa da na kiwon lafiya da ilimi da bayar da ruwan sha da kuma ayyukan inganta harkokin tattaalin arziki.

A ƙarƙashin shirin na 'SSH', an bai wa ƙungiyoyi goma tallafin dalar Amirka dubu 80, domin aiwatar da ayyuka kamar su gina azuzuwa da wuraren shan magani da wuraren sarrafa kayayyakin abinci da sayen kayayyakin ɗakunan gwaji na kimiyya da kujerun makarantun sakandare da kuma gina wuraren koyon sana'o'i.

Kungiyoyi uku kuma sun amfana da dalar Amirka dubu 60, domin aiwatar da ayyukan tsara kamma-lallen shirin wayar da kan matan kulle game da irin 'yancin da suke da shi da kuma wani taron ƙara wa juna sani na kwanaki biyu, a kan dokoki da harkokin da suka shafi cin hanci da kuma gangami game da illolin da ke tattare da yi wa mata kaciya, a yankunan jama'a har goma.

Lokacin da yake taya waɗanda suka ci gajiyar da shirin murna, Jakadan Amirka, John Campbell, ya bayyana cewa an ɓullo da shirin na SSH ne, da nufin "taimaka wa ƙungiyoyin jama'a don taimaka wa kawunansu".

A ƙarƙashin shirin taimakon kai da



*Ambasada John Campbell tare da shugabannin al'umma da ta addini da suka halarci wannan biki, har da Sarkin Kaura Namoda (mai rawani).*



*Bangaren manyan baƙi da shugabannin ƙungiyoyi da suka ci gajiyar wannan shirin*

# Rijiyar Burtsatse Ya Raya Ikpa Mbeke

"Dalar Amirka dubu tara da 386 kacal Shirin Jakadan Amirka a kan taimakon kai-da-kai (SSH) ya kashe, amma yanzu jama'ar Ikpa Mbeke na amfana da tsabtataccen ruwan sha."

Limamiyar Addinin Kirista Mother Mary Joseph Uzoigwe da ke Sashen IHM, kuma daraktar ayyuka, ta bayyana haka a lokacin da take sanya hannu a kan aiwatar da aikin na Taimakon Kai-da-kai (SSH), ranar 26 ga watan Satumba 2005.

A cewar Mother Mary Joseph, "samar da ruwan sha mai tsabta a Ikpa Mbeke ba ƙaramin aiki ba ne."

Kafin kuma a gina wannan rijiyar ta burtsatse, jama'ar ƙauyen, tare da dabbobinsu, duk suna shan ruwa ne daga gurɓataccen ruwan ƙorama ɗaya.

"Amma dalilin wannan aikin, jama'ar Amirka sun kiwata lafiyar-mu. An kuma ce lafiya uwar jiki," a cewar Rev Mother Mary.

A madadin kuma dukan Kiristoci da jama'ar ƙauyen, ta gode wa Ambasada Campbell da gwamnatin Amirka, a kan wannan karimci da ta nuna masu.

"Rev Uzoigwe ta ƙara da cewa jama'ar yankin sun gane wa idanunsu irin karimci da ƙaunar da ofishin jakadancin, tare da gwamnatin Amirka ke nuna wa talakawa da mabuƙata, ta hanyar shirin taimakon kai-da-kai na SSH".



*Bikin ƙaddamar da rijiyar burtsatse da shirin Jakadan Amirka na taimakon kai-da-kai ya gina a Ikpa Mbeke.*

Wani wakili a kwamitin aiwatar da aikin SSH, ya faɗa wa Mujallar Magama cewa, irin murna da godiyar da Mother Mary ta nuna, game da tsiran da jama'ar yankin suka yi daga shan gurɓataccen ruwan sha, ya sa dukan jama'ar yankin ke godiya da sa albarka. Haƙiƙa, kashi 75 cikin 100 na dukan cututtukan da ke addabar jama'ar yankin, daga ruwan sha marar tsabta ne, in ji shi. ■

---

kai, dole ne jama'a su ƙirƙiro ayyuka a yankunansu, dole kuma su riƙa bayar da gudummawa, gwargwadon iko, don ganin cimma nasarar ayyukan, ta fannin bayar da filaye da yin aiki ginin da kuɗaɗe da kayan aikin da duba aikin da kuma dukan abin da Allah ya huwace.

A halin yanzu ma Amirka takan bayar da gudummawar daga dalar Amirka dubu uku zuwa dubu 10, a kan kowane aiki, yayin da a shirye take ta aiwatar da ayyukan da ba su kai girman haka ba.

Jihohin da suka amfana da tallafin na wannan shekarar sun haɗa da Zamfara da Nassarawa, da Kebbi da Yobe da Kaduna da Imo da Ondo da Adamawa da Enugu da Sakkwato.

Sarkin Kauran Namoda ne ma, ya jagoranci jama'arsa a wajen wani katafaren taron da aka yi a sabon Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja. ■

# Masana'antar Markaɗa Gyaɗa Ya Ɓullo Wa Matan Zariya Da Hanyar Samun Kuɗi



*Shugabar Shirin Jakadan Amirka na Taimakon Kai, Misisi Angela Jarman, tare da matan da suka ci gajiyar wannan shiri a Zariya.*

A cikin jawabin buɗe masana'antar markaɗa gyaɗa, a Wusasa da ke Zariya, ranar 22 ga watan Satumba, Shugabar Kungiyar Taimakon Kai-da-Kai, Misisi G.L. Yahaya-Joe, ta bayyana cewa tallafin Dalar Amirka dubu tara da 121 da Jakadan Amirka ya bai wa Shirin Taimakon Kai-da-Kai na Musamman da suka ƙirƙiro, ya yi matuƙar kyautata halin rayuwar matan Wusasa, ya kuma bunƙasa yawan kuɗin da suke samu. Ga dai jawabin Misisi Yahaya-Joe, a wajen bikin:

"Tun fil-azal sana'ar markaɗen gyaɗa take da muhimmanci ga inganta irin kuɗin da jama'armu ke samu. Ba wai ma ita ce babbar sana'ar yankin ba kurum, har ma wata al'ada ce ta fitar da mai daga tunkuza, a sawwaƙe. Matanmu na da sana'o'i da dama, cikinsu kuwa har da noma, da sarrafa kayayyakin abinci da kula da gida da kuma samar da kuɗaɗen ciyar da zuri'a. Wannan shi ke janyo mana gano ƙarin hanyoyin samun kuɗi da kula da iyalanmu. Dole muna bukatar harkokin inganta fasaha na zamani, don magance waɗannan matsalolin. Don haka ƙungiyar da shugabanninta suna jiɓintar masana a fannoni da dama, tun kafin mu nemi taimakon tallafin Shirin Jakadan ga harkokin taimakon kai-da-kai (SSH). Mun kuma ji daɗi da muke cikin waɗanda suka amfana da shirin na SSH/DHRP. A gaskiya, muna godiya ga Amirka da Ambasada John Campbell da kuma shugabar shirin, Angela Jarman. Kalmar baki, ba za ta iya nuna irin farin cikin da muke da shi ba, dangane da samun wannan injin na markaɗen gyaɗa a Wusasa. An ba mu tallafin Dalar Amirka dubu tara da 121, wanda ya kai naira miliyan ɗaya da dubu 200. Da kuma waɗannan kuɗin muka sayi injunan markaɗen gyaɗar. Daga lokacin da muka samu wannan tallafin sai bukatu suka ƙara yawa. Da farko dai waɗansu jama'ar kushe mana suka yi, waɗansu kuma suka gargaɗe mu da mu bari, yayin da waɗansu suka riƙa zargin cewa za mu handame kuɗin ne. Babu abin da ba a ce ba, ko aka yi ba, don a sare mana gwiwa. Kamar kuma yadda R.W. Emerson ya ce, "sai jama'a ba su fahimce ka ba, za ka shahara". Mun yi ta ƙara turawa, domin mun yi imanin cewa muddin wannan manufa za ta sa mu shahara, to sai mun bai wa maraɗa kunya. Babu abin da zai sare mana gwiwa. Da taimkakon Allah kuma, sai ga shi mun kai ga biyan bukata a yau.

Kwanan nan muka fara wannan aikin, don haka muna sayar da man da muka sarrafa da arha. Don kuma tabbatar da ganin kowane ɗan ƙungiyar ya amfana, za a bai wa waɗanda ba su iya sayen injunan ba, bashi. Tuni ma shirin ya samar wa jama'a da dama, musamman matasa, aikin yi, a yankinmu. Ba kuma domin mata kaɗai aka ɓullo da shirin ba, sai don dukan ɗaukacin jama'ar yankin.

Hasali ma, mun gudunar da wata bitar kwana ɗaya, don ilmantar da mata maƙwabta, hanyoyin ƙara samun kuɗin shiga ta fannin sana'ar markaɗen gyaɗa.

Abun kuma tamkar mafarki ga jama'ar Wusasa, da ake ƙaddamar da wannan shirin a yau ranar 22 ga watan Satumba, 2005. Kowa ya yi farin cikin ganin jami'an Ofishin Jakadancin Amirka, da shugabar shirin, Angela Jarman. Muna godiya da wannan karimcin. ■

# "Amirka Na Girmama Addinin Kowa"
## *In ji Ambasada Campbell*

Daga Musa Ibn Mohammed
*Sashen Hulɗa da Jama'a,*
*Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja*

Jakadan Amirka a Nijeriya, ya faɗa wa Musulmin Nijeriya cewa, "Amirka tana girmama zumuncin da ke tsakaninsu" kuma "Amirka tana girmama Addininsu". Ambasada Campbell ya yi wannan jawabin ne a Sakkwato, a ranar Alhamis 13 ga watan Oktoba, a wajen buɗe bakin azumin watan Ramadan. Ya bayyana cewa, babu wani addinin da ya fi kowane cin gaba, irin Addinin Islama. Addinin Islama na ƙarfafa wa dubban miliyoyin jama'a zukata da rayuwa, cikinsu kuwa har da miliyoyin Musulmin da ke ƙasashen Amirka da Nijeriya.

Musulunci, a cewar Ambasada Campbell, zai gyara duniya. Ya kuma lura cewa, musulunci ke gyara harkokin yau da kullum na Nijeriya. Musamman ya bayyana Daular Usmaniyya da ke Sakkwato, a ƙarƙashin jagorancin Usmanu Ɗan Fodiyo da cewa wani sinadari ne na kawo canjin harkokin siyasa da wayewar hankulan ɗaukacin 'yan Nijeriya.

Ambasada Campbell ya bayyana cewa, "Daular Usumaniyya ce ta kawo canjin juyin juya-hali da ingancin ilimi da mutunta 'yancin mata da ceton talakawa daga bakin mulkin danniya".

Jakadan na Amirka ya faɗawa taron jama'ar Jihar Sakkwato, ciki har da Gwamna Attahiru Bafarawa da 'yan majalisarsa da sarakunan gargajiya da shugabannin addinai cewa, yaƙin da Ɗan Fodiyo ya yi, ya rungumi jama'a iri dabam-dabam, wanda a yau shi ne abin koyi ga al'adun jama'ar arewacin ƙasar nan, wanda ke da alaƙa da irin na Amirka.

A wajen shan ruwan buɗe bakin ne kuma, Ambasada Campbell ya iyar da saƙon Shugaba George W. Bush, a inda shugaban ya bayyana cewa "Tun farkon tarihi, Amirka ke amfana da gudummawar mabiya



*Ambasada John Campbell ya kai ziyara fadar Mai Martaba Sarkin Musulmi, Alhaji Muhammadu Maccido. Tare da shi, akwai Mrs. Claudia E. Anyaso, Shugabar Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja.*



*Ɗaya daga cikin ɗalibai daga jihar Sakkwato da suka ci gajiyar shirin musayar ɗalibai zuwa Amirka a lokacin da yake jawabi a kan amfanin wannan shiri a gare shi da kuma sauran ɗaliban da suka amfana da shirin.*

addinai da dama. Kuma Musulman ƙasarmu ne ke ƙara wa ƙasar kwarjini, muna fatan ci gaba da samun wannan karimci da ƙaunar juna, ta hanyar addinai".

Gwamnan Jihar Sakkwato, Alhaji Attahiru Bafarawa, wanda shi ma ya yi jawabi a wajen buɗe bakin, ya yaba wa irin ƙawance da taimakon da ke tsakanin Amirka da Jihar Sakkwato. Musamman ya bayar da misali da Shirin Musayar Ɗalibai (YES), wanda ya bai wa ɗaliban makarantu, da dama, damar yin karatun shekara ɗaya a Amirka. Ya kuma roƙi Jakadan da a ƙara wa ɗaliban Jihar Sakkwato gurabe.

Gwamna Bafarawa, ya kuma bayyana wa Jakadan cewa, jihar na bukatar taimakon harkokin ilimi da sanin sauran ayyukan taimako da kayayyyakin aikin Shirin Bunƙasa Damar Ci Gaban Nahiyar Afirka, don sayar wa Amirka da ƙaro.

Tun da saukarsa a Sakkwato, Ambasada Campbell ya kai ziyarar girmamawa ga Gwamna Bafarawa da Mai Martaba Sarkin Musulmi, Alhaji Mohammadu Maccido, wanda shi ne ya karɓi baƙuncin buɗe bakin, ranar Alhamis 13 ga watan Oktoba 2005. A lokacin ziyarar ne Ambasada Campbell ya bayyana lokacin da ya fara arangama da Daular Usmaniyya, tun yana ɗalibci, inda ya yi karantu game da Jihadin Daular Usmaniyya. Ya bayyana wa Sarkin Musulmi Maccido cewa, tuni yake ta hanƙoron zuwa Sakkwato, domin gane wa idanunsa irin kyawawan wallafe-wallafen da Sheikh Usmanu Ɗan Fodiyo ya yi.

A lokacin ziyarar ta kwanaki uku, Ambasada Campbell ya sanya hannu a kan Yarjejeniyar Yin Aiki da Juna



*Musayar takardar yarjejeniyar kafa ɗakin karatu na Amirka a Jami'ar Usmanu Ɗan-Fodiyo da ke Sakkwato. Daga hagu akwai Farfesa Tijjani Bande, sai kuma Mrs. Elizabeth Akibulumo, jami'ar kula da ɗakunan karatu, da kuma Ambasada John Campbell.*



*Ɗalibai, 'yammata a makaranta ta musamman a Sakkwato suna maraba da tawagar Ambasada Campbell a lokacin da ya ziyarci makarantar tare da Gwamnan Jihar Sakkwato, Alhaji Attahiru Bafarawa.*

(MOU) da Mataimakin Shugaban Jami'ar Usmanu Ɗan Fodio, wajen buɗe Ɗakin Karatu na Amirka da yin mu'amala da shirin Fulbright da ɗaliban da suka halarci Shirin YES. Ya kuma ziyarci wuraren ban sha'awa kamar su Zauren Ajiye Kayayyakin Tarihi na Waziri Junaidu, wanda ke ƙunshe da duk wani tarihi na sarakan Musulunci, tun daga Sheikh Usmanu Ɗan Fodiyo har ya zuwa ɗansa Muhammadu Bello. Ya kuma yi rangadin ayyukan ilimi da Gwamnatin Jihar Sakkwato ta yi, kamar Cibiyar Addinin Musulunci da Ilimin Kimiyya da kuma Kolejin Kimiyya da Fasaha ta Sakkwato. ■

# Ciyar Da Talakawa Da Mabuƙata A Lokacin Azumi




*Jama'a Musulmi da dama, sun halarci wannan shirin na buɗa-baki a harabar Masallacin Al-Habibiyya da ke Abuja.*

Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka ya shirya wani buɗe baki, a ranakun azumin 17 da 18 na watan Ramadan na 2005, tare da haɗin gwiwar Kungiyar Al-Habibiyya ta Nijeriya da ke babban birnin tarayya. Fiye da Musulmi 500 da waɗanda ba Musulmin ba, cikinsu har da marasa galihu da 'yan kabu-kabu suka yi hani'an da abincin da jami'an ofishin jakadancin suka raba. Shugaban Sashen Hulɗa da Jama'a, Mrs Claudia Anyaso ce ta karanta jawabin Shugaba George W. Bush, a wajen buɗe bakin, kamar yadda yake a cikin saƙon jawabin buɗe bakin Ambasada Campbell. "Ina son in sanar da ɗaukacin Musulmin Nijeriya, a wannan lokacin na buɗe baki cewa: Amirka na girmama zumuncin da ke tsakaninku da ita. Tana kuma girmma addininku."



*Jami'an Ofishin Jakadancin Amirka sun ba da gudummawarsu wajen raba abinci ga mabuƙata.*

Babban Limamin Masallacin Al-Habibiyya, Fu'ad Adeyemi, ya gode wa wannan karimcin da ofishin jakadancin ya nuna, ya kuma roƙi Musulmi da su riƙa fahimtar juna, "domin gwamnatin Amirka na nuna wa bil-Adama ƙauna, musamman Musulmi, dole mu yunƙura ga taimaka wa mabukata, a cikin wannan watan na Ramadan." ■



*Imam Fu'ad Adeyemi ne a nan a lokacin da yake hira da 'yan jaridu domin bayyana godiyarsa ga jama'ar Amirka saboda ƙauna da suka nuna ma 'yan uwa Musulmi.*



*Wani ɓangare na wannan shirin na buɗa-baki, da ke nuna yawan jami'an Ofishin Jakadancin Amirka da suka shiga sahun taimakawa.*



*Kowa da ya halarci wannan masallaci a lokacin wannan buɗa-baki na azumin babu shakka ya samu abin da zai ci.*

# Shugaba Bush Ya Kira Musulmi Su Yi Buɗe Baki A Fadarsa



*Shugaba Bush a lokacin da yake jawabi a taron buɗa-baki (Iftar) na bana da ya shirya wa al'ummar Musulmi a fadarsa da ke Washington.*

A karo na biyar ke nan, ranar 17 ga watan Oktoba, da Fadar Shugaban Amirka, Shugaba George W. Bush, ta yi tsokaci game da zimma da ƙaunar da Addinin Musulunci ke da ita. Ya kuma gode wa Musulmin duniya da suka taya Amirka yaƙi da ta'addanci.

Shugaban ya nanata jawabin waɗansu malaman Islama, waɗanda suka ce dole ne ka taimaka wa maƙwabcinka, a duk lokacin da yake da bukata. Ya ce jama'ar Amirka sun ga dil na wannan furuci, a lokacin bala'o'in guguwar Katrina da Rita.

"Duniya ta ga irin yadda Musulmi suke da karimci, da kuma ɗimbin tausayin da suka nuna, a girgizar ƙasa ta kwanan nan a Kudancin Asiya," in ji shugaban.

Shugaba Bush ya ce, dukan jama'ar Amirka na goyon

# Ranar Girmamawa Majalisar Ɗinkin Duniya

Shugaba Bush ya yaba wa majalisar a kan shekaru 60 da ta shafe tana warware matsaloli da taimaka wa duk wata yarjejeniyar taron dangi. A ranar 20 ga watan Oktoba ne, Shugaba Bush ya kira dukan Amirkawa da su yi dukan shagulgulan da suka kamata, don tunawa da Ranar Majalisar Ɗinkin Duniya, a ranar 24 ga watan Oktoba, 2005.

Bush ya ce bala'in Ambaliyar Tsunami daga Tekun Indiya, a watan Disamba na 2004 da kuma bala'o'in girgizar ƙasa a kudancin Asiya, sun nuna irin ƙaunar juna da ke tsakanin jama'ar duniya. "Irin taimakon da Majalisar Ɗinkin Duniya ta yi, ya nuna irin haɗin kan da ƙasashen duniya ke iya bayarwa, a duk lokacin da wani al'amari, mai daɗi ko mara daɗi, ya taso", in ji shi.

"Da tunani da dauriya, za mu iya cimma nasarar kare rayukanmu da mutuncin sauran jama'a", in ji shi. "Muddin muka yi haka, to za mu taimaka ga cimma burin alkawurran da muka ɗauka, a Majalisar Ɗinkin Duniya, don tabbatar da kwanciyar hankali da walwala da mutuncin da Mahaliccinmu ya bai wa bayinsa."

"Yau shekaru 60 da kafa Majalisar Ɗinkin Duniya, don ƙarin ƙwarin gwiwa da 'yanci da yaƙi da talauci da cututtuka da nufin ta taimaka ta tabbatar da 'yanci da mutuncin ɗan-Adam, a ko'ina yake. Dangane da majalisar kanta, mun ƙara jaddada kudurinmu a bisa harsashin da ya kafa ta," in ji Shugaba Bush.

Tarihi ya nuna yadda ake gwada haƙurin ɗan-Adam. Tun lokacin da aka kafa ta, bayan Yaƙin Duniya na Biyu, Majalisar Ɗinkin Duniya ta sadaukar da kanta ga warware matsalolin da suka dabaibaye duk wata harka ta ɗan-Adam. A yau, dole mu ci gaba da nuna ƙwazon samun sauƙin wahaloli da rashin 'yanci, mu kuma yi shimfidar bar wa 'ya'yanmu da jikokinmu abin gado. ■

---

bayan zaman lafiyar duniya.

"Dole mu dage ga kawo zaman lafiya, ciki kuwa har da 'yancin jama'a na gudanar da addininsu, a ko'ina suke.

Dole kuma mu yaƙi fitsarar da ake dangantawa da sunan mahaliccinmu. Na gode wa ƙasashen Musulmin da suka taimaka ga yaƙar ta'addanci, da kuma ƙasashen da suka ɗanɗana kuɗar ta'addancin."

Shugaban ya yi misali da Malamai da dama, da suka yi tir da ta'addanci.

"Na yi imanin wa'adi ne ya cika, da duk wani malamin addinin Islama, mai hankali, zai la'anci duk wata aƙidar yin amfani da Addinin Islama, domin cimma burin siyasa da wulakanta girman wannan addinin."



*Musulmai jami'an jakadanci da suka halarci bikin buɗa-baki a fadar Shugaban Kasa (White House) da ke Washington.*

Shugaban kuma ya ce yana ƙara wa Amirkawa ƙwarin gwiwar da su yawata duniya, da ziyartar Musulmai, domin su fahimci juna.

"Ina roƙon matasanmu da su koyi harshe da al'adun jama'ar yankin Gabas Ta Tsakiya. Shi ya sa a karo na farko, muka sanya Alƙur'ani a Ɗakin Karatu na Fadar Shugaban Kasar Amirka." ■

# An Kafa Harsashin Faɗaɗa Makarantar Amirka A Abuja

Daga Sani Mohammed
*Sashen Hulɗa da Jama'a,*
*Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja*

"Kisan baƙi sai gayya", wannan kuma shi ne abin da ya faru, dangane da faɗaɗa Makaratar Tarayyar Ɗaliban Ƙasashen Duniya ta Amirka a Abuja (AISA), in ji Muƙaddashin Babban Jami'in Jakadancin Amirka, Mista Thomas P. Furey, a wajen bikin aza harsashin sabon ginin makarantar na dindindin a yankin Durumi na Babban Birnin Tarayya, ranar 25 ga watan Oktoba na 2005.

Faɗaɗa ginin zai taimaka ga samar da isasshen wurin ɗaukar ɗimbin ɗaliban da ke kwarara zuwa makarantar, da kuma bai wa jama'ar yankin damar yin amfani da kaya-yyakin makarantar don bunƙasa ayyukansu.

"Muna bukatar ilimi don tsara harkokinmu na gobe da kuma tsara makomar Nijeriya, dole ne mu ilmantar da yaranmu", in ji Ministan Babban Birnin Tarayya Abuja, Malam Nasir El-Rufa'i, a wajen bikin aza harsashin.

Yau shekaru 12 ke nan da kafa Makarantar ta Amirka, a Abuja, tun ma kafin ofishin jakadancin Amirka ya taso daga Legas zuwa Abuja.

Kawo yanzu, ofisoshin jakadanci da dama sun dawo Abuja. Waɗannan ofisoshin suna ta bunƙasa, kamar dai yadda ita ma Abujar take bunƙasa, ga kuma kwararowar 'yan kasuwa da jama'ar Nijeriya da ke yawace-yawace, waɗanda ke da bukatar yaransu su yi ilimi na Amirka, irin wanda ake koyarwa a makarantar da ke Nijeriya.

Da ɗalibai 40 Makarantar ta fara, amma yanzu tana da ɗalibai 261 daga ƙasashe 40.

An shirya faɗaɗa Makarantar ce ta AISA da ginin ofisoshin daraktocin makarantar da kuma sashen gudanar da mulki, wanda bayan da aka tabka muhawarori, aka gayyaci masana harkokin gine-gine da injiniyoyin da za su sake fasalin sabuwar makarantar. Bayan da aka samu amincewar filin makarantar daga Hukumar Babban Birnin Tarayya



*Ministan Maƙamashi, Sanata Liyel Imoke yana ɗaya daga cikin manya, waɗanda suka aza tubalin ginin wannan makaranta. Sauran sun haɗa da tsohon Shugaban ƙasa, Janar Yakubu Gowon, da Ministan Babban Birnin Tarayya, Mallam Nasir El-Rufa'i, da kuma Ambasada John Campbell, da Babban Sakataren Ma'aikatar Ilimi, Alhaji Mohammed Gulma.*



*Tutocin ƙasashe dabam-dabam da waɗannan ɗaliban makaranta ke wakilta.*

Abuja, sai aka gabatar wa da Gwamnatin Amirka, wadda ta yi alkawarin taimakawa.

Daga bisani an gabatar wa Ministan Abuja da taswirar faɗaɗa ginin, wanda shi ma ya yi alkawarin bayar da fili da kuma dukan abubuwan da suka shafi aikin hanyoyi da na lantarki da kuma ruwa a harabar makarantar, tare kuma da taimakon Ambasada John Campbell, aka gudanar da wani katafaren bikin kafa asusun taimakon cimma nasarar gina makarantar, a watan Afrilun da ya wuce. Bisa ga irin waɗannan alkawurran da taimakon gwamnatoci, bayan dalar Amirka dubu 500 da aka tanada, don sayen kayayyakin, da kuma tantatsetsen zanen ginin, sai aka dumfari Hukumar Zuba Jarin Harkokin Ma'aikatu Masu Zaman Kansu na Kasashen Duniya, wanda wani sashen ne, mai zaman kansa, na Gwamnatin Amirka, don ya bayar da rancen ginin makarantar. Hukumar ta bada rancen dalar Amirka miliyan uku da dubu 250 don wannan aiki.

"Wannan kuma shi ya nuna tamkar dukan ƙasashen duniya ne suka yi dandazo, don amfanin 'ya'yanmu, a cewar Mista Furey, sa'ad da yake ambata cewa an buɗe wata sabuwar duniyar harkar inganta ilimi a Babban Birnin Tarayya.

Shugaban Hukumar Gudanarwa na Makarantar, Mista Ron Acuff, ya bayyana cewa, makarantar AISA, za ta fara karatun gaba da midil, a farkon watan Agustan 2006, yayin da Daraktar makarantar, Misisi Amy Uzoewulu ta ce makarantar ta ɓullo da wani shiri, na bayar da guraben ƙaro ilimi biyu, ga yaran Nijeriya, masu hazaƙa da basira, da ke zaune



*Zanen yadda wannan makaranta za ta kasance bayan an kammala gine-ginen.*



*Shugaban Hukumar Gudanarwa na Makarantar, Mr. Ron Acuff tare da Daraktar Makarantar, Amy Uzoewulu da wasu iyaye da ɗalibai suna aza nasu shedar wannan biki.*

a Birnin Abuja. Yaro ɗaya da budurwa ne za a riƙa bai wa wannan guraben har zuwa ga ilimin gaba da sakandare. Makarantar ta Abuja kuma tana shirya samar da guraben ƙaro ilimi ga ɗalibai biyar na yankin da ake samar da mai, na Nija-Delta.

Ministan Ilimi, wanda Babban Sakataren Ilimi, Alhaji Mohammed Gulma ya wakilta ne ta yi jagorancin wakilan Gwamnatin Tarayya a wajen bikin.

Sauran waɗanda suka halarci bikin sun haɗa da tsohon shugaban ƙasa, Janar Yakubu Gowon, da Ministan Wuta da Karafa,da Ɗan Majalisar Dattijai Liyel Imoke, da tsohon gwamnan Jihar Anambra, Cif Jim Nwobodo da iyayen yara da ɗaliban makarantar. ■

# Amfani Da Tsofuwar Dabara Ce Nasarar Aikin Tsaro A Kaduna

Daga Sani Mohammed
*Sashen Hulɗa da Jama'a,*
*Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja*

Shirin Harkokin Tsaron da Hukumar Yaƙi da Miyagun Kwayoyi ta Duniya (INL), na Shirin Koyar Da Binciken Aikata Laiffuka na Duniya (ICITAP), a karkashin Ma'aikatar Shari'a na Amirka ya tsara, ya cimma nasara a Jihar Kaduna, wajen bai wa 'yan sanda damar yaƙi da miyagun ɗabi'u da sauransu. Shirin na koyar da 'yan sanda da ƙungiyoyi masu zaman kansu da shugabanni, sanin muhimmancin harkokin fahimtar yunƙurin hana aikata laifi.

Manajan Shirin na ICITAP, Mista Eric Beinhart, ya bayyana cewa shirin , wani haɗin gwiwa ne tsakanin jama'a da 'yan sanda wanda Sufeto-Janar na 'yan sanda, Mista Sunday Ehindero ya amince da shi.

"Shirin zai taimaka wa al'umma sanin irin gudunwamar da za su bayar wajen tsaron ɓangarorinsu. Wannan kuma wata manufa ce ta ƙasa baki ɗaya, wadda ta ƙunshi kuratan 'yan sanda da jami'ansu, amma aka yi amfani da Jihar Kaduna, don zama zakaran gwajin dafi", in ji Mista Beinhart.

Manufar shirin ICITAP ita ce don taimaka wa 'yan sanda ga aiwatar da aiki yadda ya kamata, da zama rundunar da ke yi wa jama'a aiki da kare lafiyarsu da mutuncinsu. Shirin na amfani da kekuna wajen rangadi, domin shiga lunguna. Rangadi da kekuna, ya samo asali, sai dai a ce an wuce zamaninsa. Yana taimakawa



*Mataimakin Gwamnan Jihar Kaduna, Mr. Patrick Yakowa tare da Jami'an Wannan Shiri, John da Larry.*



*Jami'an Kwamitin Hulɗa Tsakanin Al'umma da 'yan sanda a lokacin da suke taronsu a Kawo, Kaduna. Sun yi alƙawarin gyara ofishin 'yan sanda na wannan unguwa.*

matuƙa wajen karaɗe dukan yanki, da ganin irin abubuwan da jama'ar yankin ke yi. An samu gagarumar nasarar da jama'ar Kaduna suka yaba, domin an rage yawan ɓarnar kuɗin gyaran ababen hawa. Shirin na Hukumar INL somin-taɓi ne ga wani gagarumin shirin da Kasar Ingila ke aiwatarwa a Nijeriya. Lokacin kuma da Gwamna Ahmed Mohammed Makarfi ya ji irin nasarar da shirin ke samu, sai ya ƙara agaza wa shirin da kekuna 250.

Manufar shirin na ICITAP shi ne don taimaka wa manufofin babban ofishin gwamnati da sashen shari'a na Amirka da ƙasashen duniya, ta hanyar taimaka wa gwamnatocin ƙasashe masu tasowa, wajen wadata su da ƙwarewar aiwatar da dokoki a tafarkin dimokuraɗiyya da shirin 'yancin ɗan Adam.

Maƙasudin harkokin koyarwa da taimakon da shirin na ICITAP ke bayarwa shi ne don inganta ƙwarewa ga cibiyoyin aiwatar da dokoki na jama'a. An kuma tsara bayar da taimakon don:

* Inganta ƙwarewar gabatar da binci-ke da bin diddigin shaidar aikata laifi.
* Taimaka wa ga inganta ilimin masu koyarwa da na irin dokokin da jami'an za su aiwatar.
* Inganta harkokin mulki da gudanar da al'amurran hukumomin aiwatar da dokoki, musamman irin kuzarinsu na ci gaba da horar da ma'aikata da ladabtar da su.
* Inganta dangantakar da ke tsakanin 'yan sanda da jama'ar da suke yi wa aiki.
* Samarwa ko ƙarfafa zuciyoyin masu kai farmaki ga sababbin laiffuka da al'amurran da suka shafi dokokinsu. ■



*Shugabannin wannan shirin na haɗin gwiwa. Daga hagu: Eric Beinhart, da Reberen Sam, da John, da Larry, da kuma jami'in'yan sanda, Daniel.*




*'Yan sanda a lokacin da suke sintiri a kan kekuna daga kwalejinsu da ke cikin garin Kaduna zuwa Kurmin Mashi, a bayan gari.*

# Taimaka Wa Waɗanda Bala'in Katrina Ya Jigata




*Tawagar 'yan majalisun Jihar Iowa da suka kawo ziyara Nijeriya a lokacin da suka ɗauki hoto kusa da babban katin jajentawa da ƙungiyoyi dabam-dabam suka sanya hannu a kai domin nuna tausayi ga ƙasar Amirka da al'ummarta da wannan bala'i ya jigata.*

Ranar 15 ga watan Satumbar 2005 ne, aka yi wani cincirindon da ba a taɓa yi ba, a zauren taro na Sashen Hulɗa da Jama'a, domin ya zarce taron da akan yi da manema labarai, a duk ranakun Alhamis. Babu kujerar da babu ɗan-Adam, a lokacin da Shugabar sashen na hulɗa da jama'a, Claudia Anyaso ta gabatar da taken makon a kan "Koƙarin Farfaɗowa Daga Bala'in Guguwar Katrina".

A lokacin jama'a sun saduda, inda 'yan Nijeriya suka riƙa zubar da hawaye, don tausaya wa Amirka game da mummunan ta'adin da guguwar ta "Katrina" ta yi mata. Claudia ta karanta jawabin Shugaba Bush, a inda yake gode wa mutanen ƙasashen duniya game da gudummawa da agajin da suka bayar. Ta bayyana yawan ɓarnar da aka yi, ta kuma musanta irin raɗe-raɗin da ake yi na cewa, wai gwamnati ta ƙi kulawa da sauri domin mazauna yankin na New Orleans baƙar fata ne.

Kungiyoyi biyu na Nijeriya suka fara gabatar da kansu, don neman tara kuɗin taimakawa, yayin da wata Kungiyar Bunƙasa Ci Gaban Harkokin Duniya da ke yankin Mississippi, na Amirka (MCID), ta nuna ƙudurinta na haɗa gwiwa don gudanar da harkar agajin, a Nijeriya.

Daraktan ƙungiyar, a Nijeriya, Keith A. Benson Snr. ya bayyana cewa wakilan majalisu da sauran masu faɗa a ji, a Nijeriya, a shirye suke kan jiɓintar takwarorinsu na Amirka, don aiwatar da shirin na ƙungiyar MCID. Ya ce MCID ta horar da wakilan majalisun jihohi 13 na Nijeriya, don taimaka wa mulkin dimokuraɗiyya, kuma waɗannan wakilan da sauran manyan mutane suna da alaƙa da jama'ar Mississippi da New Orleans da Alabama.

Wani sanannen ma'aikacin gidan rediyon Cool FM, Mr. Wale Ewedemi, ya bayar da shawarar ajon

"Afirka don Amirka", a inda jama'a za su riƙa buga waya zuwa ga gidan rediyon, tare da haɗin gwiwar kamfanonin tarho, don bai wa talakan Nijeriya damar bayar da gudummawar Naira 100 kowanensu, ga waɗanda bala'in guguwar na Katrina ya shafa.

Ita kuma Kungiyar Kula da Muhalli ta Afirka, mai zaman kanta, (African Environmental Action Network), wadda ke bayar da shawarwari da horar da masu aikin ceto, ta bayyana shirinta na tara mawaƙa, tare da haɗin gwiwar Kungiyar Makaɗa da Mawaƙa ta Nijeriya, (PMAN). Wakiliyar ƙungiyar, Miss Eferemo, ta ce tuni aka kammala shirye-shirye da Bankin ECO, don bayar da gudummawar ta Asusun Tallafa wa Bala'in na Katrina, ta kuma roƙi 'yan Nijeriya da su agaza. ■



*Mrs. Caludia E. Anyaso, Shugabar Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka.*



*Mr. Keith A. Benson Snr., shugaban MCID a Nijeriya, a lokacin da yake jawabi a kan irin gudummawa da 'yan Majalisa ke son bayarwa ga al'ummar Amirka da wannan bala'i ya jigata.*



*Ɗaliban Kungiyar Masu Karatun Harkokin Majalisar Ɗinkin Duniya sun kawo nasu ɗauki ga al'ummomin Amirka da bala'in Katrina da Rita suka jigata.*

# Taimakon Agajin Guguwar Katrina Da Rita

"Haɗa Kan Kasashen Duniya Don Aiki Tare". Wannan shi ne taken Kungiyar Matasan Nijeriya na Majalisar Ɗinkin Duniya (UNYA), a ƙarƙashin jagorancin Shugaba Fakayode Oluwatobi. Jami'ai 15 na ƙungiyar UNYA sun kai ziyarar ban girma a Ofishin Jakadancin Amirka, da ke Abuja, a ranar 27 ga watan Oktoba, don zama wani ɓangare na tunawa da shekaru 60 da kafuwar Majalisar Ɗinkin Duniya. Domin kuma tausaya wa waɗanda Guguwar Katrina da Rita suka yi wa ɓarna. Jami'an na UNYA sun bayar da wani katin tausayawa, da ɗaliban Nijeriya dubu ɗaya suka sanya wa hannu. An ƙaddamar da Kungiyar ta UNYA ne a watan Agusta na 2000, a Jami'ar Obafemi Awolowo da ke Ife ta Jihar Osun, wanda a halin yanzu tana da rassa 20, a jami'o'in Nijeriya.



*Wakilan Kungiyar Ma'aikata 'yan Nijeriya da ke aiki a Ofishin Jakadancin Amirka sun ba da nasu gudummawa ga mataimakiyar Sakatariyar Harkokin Waje Mai Kula da Nahiyar Afirka, Dr. Jendayi Frazer, a lokacin da ta kawo ziyara Nijeriya.*

Bugu da ƙari, Shugaban Kwamitin Bayar da Shawarwari ga Ma'aikatan Aikin Jakadanci (FSNs), Mukhtar Shitu, ya jagoranci wakilai bakwai na Kungiyar ta FSN, daga sassa dabam-dabam da ke ƙarƙashin Ofishin Jakadancin Amirka na Nijeriya, domin gabatar da katin jajentawa ga Ambasada Campbell, don nuna tausayawarsu ga waɗanda Guguwar ta Katrina ta yi wa ɓarna.

Lokacin da yake karɓar katin, Ambasada Campbell ya bayyana cewa, "Wannan karimci ya sanyaya mini zuciya. Zan kuma isar da saƙonku zuwa Birnin Washington, ta hannun Gwamnan New Orleans, domin nuna juyayinmu ga jihar. ■

# Dokta Frazer Ta Sako Kafa Afirka A Matsayin Mataimakiyar Sakatariyar Gwamnatin Amirka



*Ambasada John Campbell ne ke gabatar da manyan Ma'aikatan Ofishin Jakadancin Amirka ga bakuwar, Dr. Jendayi Frazer. A hagu, akwai Mr. Russel Hanks, Babban Jami'i a Fannin Siyasa.*

Dokta Jendayi Frazer ta kawo ziyarar farko Afirka, a matsayin Mataimakiyar Sakatariyar Harkokin Kasashen Waje, mai kula da Harkokin Afirka, a cikin watan Oktobar 2005. Ta iso Nijeriya ne, dab da lokacin da aka bayar da rahoton cewa jirgin Kamfanin Bellview ya faɗi, ga kuma labarin mutuwar uwargidan Shugaban Kasa, Stella Obasanjo.

Wannan ziyarar ta ba ta damar kai gaisuwar ta'aziyya ga Shugaba Obasanjo, ta kuma nuna juyayinta

# Shirin Taimaka Wa Yaƙi Da Miyagun Kwayoyi.

Jakadan Amirka, John Campbell da Babban Mai Shari'a, kuma Ministan Shari'a, Cif Bayo Ojo, sun sanya hannu a kan wata babbar yarjejeniyar gudum-mawar Dalar Amirka miliyan ɗaya da dubu 552, a ƙarƙashin Shirin Taimaka Wa Yaƙi Da Miyagun Kwayoyi. Hukumomi huɗu daga Nijeriya, wato Hukumar 'Yan Sanda da Hukumar Yaƙi da Tilasta Hana Yin Amfani da Miyagun Kwayoyi (NDLEA) da Hukumar Laiffukan Cin Hanci da Rashawa da Laifuffukan da suka Danganci Haka (ICPC) da kuma Hukumar Laiffukan Tattalin Arzikin Kasa da Kuɗaɗe (EFCC), suna cikin hukumomin da za su amfana da shirin. ■



*Ministan Shari'a, Mr. Bayo Ojo SAN, tare da Ambasada John Campbell ne suke sa hannu a yarjejeniyar taimakon.*

ga waɗanda suka rasa 'yan uwansu a haɗarin jirgin na Bellview.

Lokacin da take jawabi ga 'yan jaridu, ranar 24 ga watan Oktoba, bayan ta kai ziyarar a Fadar Gwamnati, Mataimakiyar Sakatar-iyar ta jajenta wa 'yan Nijeriya game da haɗarin jirgin, a inda ta ce "Ina mai jajentawa da ta'aziyya ga Shugaba Obasanjo da iyalansa, game da rashin Uwargida Stella Obasanjo. Ina kuma miƙa ta'aziyyata ga iyalan waɗanda suka rasa masoyansu a haɗarin jirgin Bellview da ya faɗi a Ifo."

Dokta Frazer ta tabbatar da cewa Babban Jami'in Tsaron Ofishin Jakadancin , Manjo Joseph Haydon, ya na cikin wannan jirgi da tayi haɗarin.

Kafin kuma ta iso Nijeriya, Dokta Frazer ta ziyarci ƙasashen Laberiya da Gana da Tanzaniya. Har ila yau, ta ziyarci Afirka ta Kudu, a inda ta taɓa zama jakada, daga watan Agusta na 2004 zuwa watan Yuli na 2005.

Shugaba George W. Bush ne ya bai wa Dokta Jendayi Frazer wannan muƙamin, ranar 17 ga watan Yunin bana.

Majalisar Dattijan Amirka kuma ta tabbatar da naɗinta, ranar 29 ga watan Yuli, 2005 ɗin nan. ■

# Ɗalibai Sun Bi Sahun Manyan 'Yan Nijeriya

Daga
Idika U. Onyukwu



*Ɗalibai daga Makarantu dabam-dabam a lokacin da suke neman ƙarin bayani a kan hanyoyin shiga jami'o'in Amirka.*

"Ilimi mai nagarta ne zai buɗe wa matasan Nijeriya hanyoyin tsara rayuwarsu don gobe". Jakadan Amirka a Nijeriya, John Campbell ya ce haka ne, a lokacin da yake bayyana matsayin ilimi, a wajen Baje Kolin Ilimi na Cibiyar Bayar da Shawarwari Game da Ilimi, (EAC), na bakwai, da aka buɗe a Abuja da Legas, a ranakun 5 zuwa 7 ga watan Oktoba, 2005.

Jama'a masu ɗimbin yawa daga wasu birane kamar su Zariya da Jas, suka halarci bikin baje kolin na bana, a Abuja, yayin da jama'a daga Badun da Abekuta suka halarci na Legas.

A cikin jawabin buɗe taron, Ambasada Campbell, ya ce mafi yawan ɗaliban da suka halarci bikin na bana, daga manyan makarantu da dama su ke bin hanya mafi dacewa, ta yin "koyi da jerin gwanon manyan 'yan Nijeriya da suka yi karatu a Amirka", kafin su zo don bayar da tasu gudummawar ga ƙasarsu.

Jakadan ya ambaci waɗansu daga cikin 'yan Nijeriya, kamar su shugaban jumhuriya na farko, Dokta Nnamdi Azikiwe da Ministan Kimiyya da Fasaha, Farfesa Turner Esoun da Gwamna Donald Duke na Jihar Cross Riba da Babban Daraktan Harkokin Saye da Sayarwa, Ndi Okereke-Onyiuke. Jakadan kuma ya ambaci ayyukan Oby Ezekwesili a "Hukumar Bin Diddigi", da Ministan Albarkatun Ƙasa, Inginiyan Na'ura Mai Ƙwaƙwalwa, Philip Emegwali da Ministan Karafa da Wutar Lantarki, Ɗan Majalisar Dattijai Liyel Imoke, don zama wata ƙwaƙƙwarar hujjar irin danƙon zumuncin harkokin ilimi da ke tsakanin Nijeriya da Amirka.

Fiye da shekaru 40 ke nan, da jami'o'i da kolejojin Amirka ke halartar irin wannan bikin. Folu Ojutalayo na Jami'ar Huron ta Amirka da ke London da Hakeem Tijjani na Jami'ar St. Francis da Maren Miligan da ke Yankin Maryland, suka yi wa ɗaliban da suka ƙware tambayoyi, nan take.

Bikin kuma ya bayar da wata kafar da jami'an hulɗar jakadancin Amirka da ɗalibai da iyayen yara suka tattauna, don magance matsalolin da suka shafi bayar da iznin shiga ƙasa da kuma tunanin ɗaliban da ke karatu a Amirka, game da bala'in ta'addanci na 11 ga watan Satumba.

Wani ba amirke, ɗan asalin Nijeriya, kuma Shehun malami da ya ci gajiyar Shirin Musayar Ɗalibai da Malamai "Fulbright", Dokta Emeka Okoli ya gabatar da wata ƙasida mai taken "Nazari A Kan Amirka Dangane da Buɗe Kofar Bayar Da Ilimi Ga Kasashen Duniya", ya bayyana cewa, sakamako mai kyau, tun daga Jarrabawar Hukumar Jarrabawa ta Yammacin Afirka, ta makarantar sakandare, shi ne tushen neman ilimi a Amirka.

"Muddin ka ci jarrabawa, ka kuma bi ƙa'idar cike takardar neman shiga jami'a, to sauran mai sauƙi ne", in ji Okoli.

Dalilin kafa Cibiyar Bayar da Shawarwarin Ilimin dai shi ne don taimaka wa 'yan Nijeriya su ƙara samun ilimin manyan makaratu a Amirka, da bayyana masu duk wata

masaniya game da tsarin ilimi a Amirka. Masu bayar da shawarwari a cibiyar kuma sukan tattauna da ɗalibai don bayyana masu irin fannin ilimin da ya kamata su ɗauka, da kuma jami'o'in da suka kamata su je.

Kowace shekara, masu bayar da shawarwari na Cibiyar ta EAC suna ganawa da ɗalibai fiye da dubu 20. Shirin Wayar Da Kan Jama'ar na ganawa da ɗalibai a ranar Talata da kuma ranar Laraba. Aƙalla ɗalibai 300 ke zama wakilai, bayan sun kammala cike takardun samun makarantu da kolejoji, a Amirka. Bayan samun shiga makarantun, da dama sukan sami tallafin kuɗi ta Shirin Cibiyar ta EAC. A wannan shekarar ajin kolejin koyon kamun kifi da waɗanda suka sauke karatu sun samu jimlar kuɗi Dalar Amirka miliyan ɗaya da dubu 500, a fannin gurbin ƙaro ilimi da talla-fin kuɗi daga jami'a. Babu shakka, Cibiyar ta EAC na share hawaye ga duk wani ɗalibin da ke da ƙoƙarin yin karatu a Amirka, kuma halartar bikin cibiyar a kowace shekara ne, masomin biyan bukata. ■

# An Buɗe Cibiyar Amirka A Kaduna

Daga
Idika U. Onyukwu



*Mai Girma Gwamnan Jihar Kaduna, Alhaji Ahmad Muhammad Makarfi ne a nan tare da Mrs. Claudia E. Anyaso ( a damansa) da kuma Mr. Henry Mendelsohn, Jami'in kula da ɗakunan karatu na Amirka a shiyyar Afirka ta Yamma.*

Ranar 27 ga watan Satumba ne, Gwamnan Jihar Kaduna, Alhaji Ahmed Mohammed Makarfi, da kwamishinoninsa, tare da haɗin gwiwar Shugabar Sashen Hulɗa da Jama'a, ta Ofishin Jakadancin Amirka, Claudia Anyaso, suka buɗe ɗakin karatu na Amirka, a Cibiyar Bunƙasa Harkokin Mata da ke Kaduna. Wannan cibiyar, ita ce ta shida, a cikin jerin cibiyoyin wayar da kan jama'a da Ofishin Jakadancin Amirka ya buɗe, don faɗakar da 'yan Nijeriya game da duk waɗansu bayanai game da Amirka.

Lokacin da take jawabi, Misisi Anyaso ta ce, cibiyar za ta riƙa "biyan muradin masu bukatar yin hulɗa da jama'a da sanin al'adun Amirka, domin gano waɗansu harkokinsu da tunaninsu don sanin yadda za a zauna tare".

Da yake mayar da jawabi, Gwamna Makarfi ya bayyana cewa, kafa wannan cibiyar a Kaduna, wani ƙarin danƙon zumunci da 'yan-uwantaka ne, tsakanin Ofishin Jakadancin Amirka da jama'ar jihar. Gwamnan ya ce a matsayin jihar na mazaunin harkokin ilimi da koyar da shi, a yankin Arewacin ƙasar nan, "ba ƙaramar dabara ba ce, da aka buɗe cibiyar a Kaduna".

A ƙarƙashin yarjejeniyar kafa ɗakin karatun na Amirka a wannan cibiya da ke Kaduna, Sashen Hulɗa da Jama'a na Ofishin Jakadancin Amirka zai riƙa bayar da litattafai da faya-fayai da mujallolin tarihi da rubuce-rubuce na harkokin ilimi da al'adu da kuma shari'a na Amirka. Kazalika da kayayyakin bayar da shawarwarin koyar da ilimi na Dalar Amirka dubu takwas, yayin da Cibiyar Bunƙasa Harkokin Jama'ar Kaduna za ta bayar da wuraren ajiyar waɗannan kayayyaki. Ɗakin karatun na Amirka da ke Kaduna, za ta taimaka wa marubuta da 'yan jaridu da masu fafutukar neman 'yancin jama'a da ɗalibai da manyan malaman ilimi da duk wani mutum ko ƙungiya da ke da sha'awar yin karatu a Amirka. Kyauta cibiyar za ta gudanar da harkokinta ga duk wanda ke bukata a ciki da wajen Jihar Kaduna. ■

Zuwa ga Editan Magama,

Bayan gaisuwa da fatan alheri zuwa gare ka da sauran ma'aikata, bayan haka ina so in nuna farin cikina da ganin wannan mujallar a hannun wani basaraken gargajiya.

Ina kuma mai farin cikin gabatar maka da ra'ayoyina domin dubawa. Ra'ayoyin kuwa su ne, Mujallar tana ilimantarwa ga ta kuma da tsari mai ma'ana, wanda aka tsara a cikin alkalumma masu kyau.

Daga ƙarshe, ina fatar za a riƙa aiko mini da wannan mujallar, a adireshin da na rubuta, da fatar Allah kuma ya ɗaukaka wannan mujallar, amin.

Ni ne Naku,
Malam Kawu Hamid,
Azare. Jihar Bauci.

Zuwa ga Edita,

Bayan gaisuwa mai yawa da fatan kuna lafiya, bayan haka, ina mai farin cikin sanar da kai cewa na ga mujallarku ta fitowar watannin Yuni da Yuli na 2005, a Kaduna, lokacin da na ziyarci wani aminina.

Na ga hoton Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja, na kuma karanta waɗansu bayanai da suke nuna irin taimakon da ofishin ya yi, na kafa Cibiyar Tara Jini mai Tsabta da kuma wayar da kai game da yaƙi da cutar ƙanjamau da kuma shirin taimaka wa ɗaliban Nijeriya, wajen ƙaro ilimi.

Bugu da ƙari, na fahimci irin taimakon da Amirka ke son yi, wajen cike giɓin fasaha da fahimtar al'adun Amirka da dai sauransu.

Ina fata Edita zai tuna da ni cikin waɗanda ke bukatar a riƙa aiko masu da wannan mujallar, a duk fitowa.

Ni ne naka,
Malam Aliyu Hassan,
Tudun Wada,
Zariya.

Zuwa ga Edita,

Bayan gaisuwa na rubuto wannan wasikar ne don in bayyana maka irin sha'awar da nake da ita ga Mujallar Magama, lokacin da na karanta ta, a hannun ɗaya daga cikin abokaina.

Na fahimci abubuwa da dama game da harkokin Amirka, kamar tallafa wa ɗalibai masu hazaƙa, wajen ƙaro ilimi da illolin cutar ƙanjamau da rigakafin kamuwa da ita, kazalika da rashin nuna wa mutanen da suka kamu da ita ƙyama, ko bambanci.

Bugu da ƙari mujallar na faɗakar da jama'a game da jahilcin rashin fahimtar harkokinta da shirye-shiryen gwamnatin Amirka, don ci gaban al'umma.

Ina kuma jajenta wa al'ummar Amirka dangane da bala'in guguwa da ambaliyar da Guguwar Katrina ta haddasa.

Daga ƙarshe, ina bukatar da ku fara aiko mini da wannan mujallar, mai farin jinni, a duk lokacin da kuka wallafa.

Ni ne naku,
Malam Abba Mustapha Yola,
Jahun. Jihar Jigawa.

Zuwa ga Edita,

Gaisuwa mai yawa tare da fatar alheri.

Dalilin wannan wasiƙar shi ne in sanar da kai cewa ni makarancin mujallarku ce ta Magama wanda sonta ya shiga zuciyata matuƙa.

A ƙarshe, ina bukatar da a riƙa aiko mini da kowace fitowa kuka yi na wannan mujallar.

Ni ne naku,
Malam Aliyu Haliru Midila,
Yola,
Adamawa State.

***Kuma zaku iya karanta mujallarmu a intanet. Don haka, ku aiko mana da adireshi ku na e-mail a wannan adireshi:*** magama-ng@lists.state.gov ***domin mu rika aiko muku da mujallarmu kai tsaye a duk lokacin da muka fito.***

## RA'AYINKA

Idan ka samu mujallar *Magama,* muna bukatar ra'ayinka game da ita.
Suna ..................................................
..........................................................
Adireshi na e-mail.............................
..........................................................
..........................................................

Za'a iya aiko mana da wasiƙu ta hanyar e-mail a wannan adireshi: magama@state.gov

*Ka aiko mana da dukan bayanai ta hanyar e-mail ko kuma akwatin gidan waya mai lamba: 5760 Garki, Abuja.*

e-mail zuwa ga edita: magama@state.gov

# KAWAR DA CUTAR KANJAMAU!
# KAWAR DA CUTAR KANJAMAU!!
# KAWAR DA CUTAR KANJAMAU!!!

# KALAC 2005

*Kaurace wa jima'i, sai ka yi aure

*Kada ka cutar da abokin auratayyarka

*Tausaya wa masu ɗauke da ƙwayoyin cutar ƙanjamau ko cutar

*Idan ba ka iyawa, to yi amfani da kororon roba

**Kada Ka Tsorata!** Je A Gwada Ka, Don Sanin Ko Kana Da Cutar Kanjamau, Ko Ka Nemi Shawara

Kungiyar Matasan Nijeriya tare da haɗin gwiwar Ofishin Jakadancin Amirka a Nijeriya ke gabatar da wannan, ta hannun Shirin Wayar da Kai na shirin Asusun Agajin Gaggawa don Taimakawa Masu cutar Kanjamau PEPFAR

*Domin neman ƙarin bayani, ko shawarwari, ko bayyana ra'ayinka, tuntuɓi*

email: youthsinnigeria@hotmail.com, youthsinnigeria2000@yahoo.co.uk

Ko lambar tarho: 08036158542 Efax: 1-708-810-3390

PRESIDENTIAL EMERGENCY PLAN FOR AIDS RELIEF
UNITED STATES MISSION IN NIGERIA

## Kungiyar Tsofaffin Shirin Musayar Ɗalibai Da Malamai "Fulbright" Ta Nijeriya (FAAN)

### Tana sanarwa game da

# KANO 2006

## TARONTA NA HUƊU

A ranakun 15 zuwa 18 ga watan Fabrairu, 2006.
A Harabar Jami'ar Bayero, Kano
*Tana kuma kiran da a gabatar da ƙasidu a kan*

**Taken:**

"Dangantakar Nijeriya da Amirka Game da Fuskantar Kalubalan Fahimtar Juna A Karnin Da Za Mu Shiga"

## Nuwamba 2005

| Sun | Mon | Tue | Wed | Thu | Fri | Sat |
|---|---|---|---|---|---|---|
| | | 1 | 2 | 3 | 4 | 5 |
| 6 | 7<br>Shirin Bita: Mataimakiyar Mai Bayar da Shawara A Kan Ilmi, Shade Adebayo za ta je Jihar Gombe, a bisa ga gayyatar da Ma'aikatar Ilmi ta Jihar ta yi mata. | 8<br>Shirin Bita: Mataimakiyar Mai Bayar da Shawara A Kan Ilmi, Shade Adebayo za ta je Jihar Gombe, a bisa ga gayyatar da Ma'aikatar Ilmi ta Jihar ta yi mata. | 9<br>Shirin Bita: Mataimakiyar Mai Bayar da Shawara A Kan Ilmi, Shade Adebayo za ta je Jihar Gombe, a bisa ga gayyatar da Ma'aikatar Ilmi ta Jihar ta yi mata. | 10<br>Bayani ga 'yan jarida.<br>Alowai bayanin da Stewart da Obiaka, za su yi wa 'yan jarida. | 11 | 12 |
| 13 | 14<br>Makon Harkokin Ilmin Kasashen Duniya: a Cibiyar Bayar da Shawarwari, ta Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja.<br>Alowai lacca mai taken: "Tabbatar Damar Samun Ilmi A Kasashen Duniya." Sai kuma laccar da Misis Akinbode Agboeye na Hukumar Jami'o'in Nijeriya, zai bayar game da Yadda Za a Gayyato Nijeriya Ta Hanyar Yin Karatu A Kasashen Ketare. Da kuma laccar da Dakta Daniel Obaka na Cibiyar Bayar da Shawarar Ilmi na Ofishin Jakadancin Amirka, zai bayar game da Dangantakar Hadi Kan Juna ta Hanyar Musayar Dalibai. Alowai kuma Shirin Musayar Matasa da Dalibai (YES) da Daukan Sashen Musayar Matasa da Dalibai ta Kasa, Dokta Sinds, zai yi bayani a kai. | 15<br>Makon Harkokin Ilmin Kasashen Duniya: a Cibiyar Bayar da Shawarwari, ta Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja.<br>Za a kai ziyara a makarantun sakandare da dama da ke Jihar Kaduna. Makarantun kuwa su ne: Kolejin Zamani da Kolejin Essence da Kolejin Grammatin Tarayya da kuma Dalibai Sashen Zane-zane da Halayyar Dan Adam, na Jami'ar Ahmadu Bello da ke Zaria. | 16<br>Makon Harkokin Ilmin Kasashen Duniya: a Cibiyar Bayar da Shawarwari, ta Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja.<br>Bude Zaure don tattaunawa a kan "Karatu a Amirka", a inda kuma za a gudanar da shirin baje kolin kayayyakin koyarwa daga jami'o'in Amirka da kuma zantawa da iyayen yara da dalibai. | 17<br>Makon Harkokin Ilmin Kasashen Duniya: a Cibiyar Bayar da Shawarwari, ta Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja.<br>Hira da 'yan jarida a kan a'Farancan ahinai wai gina jiki, a Nijeriya.<br>Shirin Ziyarar Shugabanni daga Kasashe: Daraktan Kula da Mahalli, na Ma'aikatar Mahalli ta Jihar Legas, Misis Oluwatoyin Onisarotu, zai yi jawabi game da "Aikatattun Mahalli." Sai kuma Masanin Mai Bayar da Shawara ga Asusun Kula da Halittun Rewa, a Fadar Shugaban Kasa, da ke Abuja, Misis Ahmad D. Sanda da zai yi jawabi a kan "Al'amuran Mahalli a Birane."<br>Za a kai ziyara ga Makarantar Sakandaren Kimiyyar 'Yammata da ke Kogi. | 18<br>Makon Harkokin Ilmin Kasashen Duniya: a Cibiyar Bayar da Shawarwari, ta Ofishin Jakadancin Amirka da ke Abuja.<br>Za a nuna majigi a kan abin da ya shafi Harkokin Ilmin Kasashen Duniya. | 19 |
| 20 | 21 | 22 | 23 | 24<br>Bayani ga 'yan jarida, dangane da Asusun Agajin Gaggawa na Shugaban Kasa don tamaika wa masu cutar Kanjamau, AIDS da kuma sauransu harkokin da aka shirdida don rage yaduwa da cutar Kanjamau ta Duniya. | 25 | 26 |
| 27 | 28 | 29 | 30 | | | |

Wallafar Ofishin Jakadancin Amirka, Nijeriya